# TASKOKIN ILIMI

## Sama da TAMBAYOYI 100 da AMSOSHINSU

### A Akida da Tarihin Annabi da Zikirori




5 Matakai

Bugu na biyar


Tattarawa da hadawar:
**Salahuddin bin Abdussalam Al'ubaidi**
Allah Ya gafarta masa da iyayensa

بسم الله الرحمن الرحيم

# Da sunan Allah
# Mai Rahama Mai jinƙai


**Taskokin Ilimi**

Sama da Tambayoyin ɗari da Amsoshinsu
na Aƙida da Tarihin Annabi da Zikirori

Sunan marubuci: Salahuddin Abdussalam Al'ubaidi
Sunan mai bugawa: Alkunuzul Asariyya

**Bugu na biyar: 2024**

**Ma'aikatar tsarin lambobin littaffi na duniya ta ƙasar Libiya**

**Bugawan Darul Kutub Alwaɗaniyya/Bingazi/Libiya**

**Lambar rara: ISBN 7-3-9696-9959-978**

**Lambar ajiya ta doka: 585/2023**

**9097074–9096379–9090509**

**nat_lib_libya@hotmail.com**

# Abubuwan da ke ciki


Gabatarwa: .................... 04

Mataki na Farko .................... 06

**Aƙida** .................... 07

Tarihin Annabi ﷺ .................... 18

Zikirori na shari'a: .................... 24

Mataki na biyu .................... 29

**Aƙida** .................... 30

Tarihin Annabi ﷺ .................... 41

Zikirori na shari'a: .................... 49

Mataki na Uku .................... 56

**Aƙida** .................... 57

Tarihin Annabi ﷺ .................... 68

Zikirori na shari'a: .................... 74

Mataki na huɗu .................... 81

**Aƙida** .................... 82

Tarihin Annabi ﷺ .................... 94

Zikirori na shari'a: .................... 103

Mataki na biyar .................... 110

**Aƙida** .................... 111

Tarihin Annabi ﷺ .................... 126

Zikirori na shari'a: .................... 138

# Gabatarwa:

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jinƙai
Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai, daɗin tsira da aminci ya tabbata ga Annabinmu Muhammadu cikamakin Annabawa, da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi bayansu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako. Bayan haka:
Haƙiƙa Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana bin salo iri-iri wajen karantar da Sahabbansa, daga cikin salo da yake bi akwai salon tambaya da amsa, saboda abin da wannan salo yake ɗauke da shi na sanya shauƙi da wasa ƙwaƙwale, da tabbatar da ma'ana ta hanya mafi kyau.
Misalin haka shi ne Hadisin Mu'azu Allah Ya ƙara masa yarda cewa: Lallai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce da shi: ((Ya kai Mu'azu; Shin kasan mene ne haƙƙin Allah a kan bayi, da kuma haƙƙin bayi a kan Allah)). Ya ce: Sai na ce: "Allah da ManzonSa su suka fi sani".
Lura da wannan ya sa na rubuta wannan littafin a bisa tsarin tambaya da amsa, kuma na sa masa suna **"taskokin ilimi ga yara". "Sama da tambayoyi ɗari da amsoshi na Aƙida da Tarihin Annabi da Zikirori"**, kuma na kasa littafin zuwa kashi uku: Aƙida, Tarihin Annabi, da Zikirori na shari'a, ta yadda uba da uwa masu daraja za su iya karantar da 'ya'yansu ta hanya mai banƙaye kuma mai kyau, wacce za ta zama mafi

sauƙin haddacewa, kuma na yi ƙoƙarin na ga cewa na kawo dalilai na shari'a ga kowane abin da na kawo, da kuma fatawowin malamai nagartattu.

Ya kai uba mai daraja, ya ke uwa mai tarbiyantarwa, duk abin da aka samu a wannan littafin na daidai da fa'ida, to, daga Allah ne Shi kaɗai, duk abin da kuma aka samu na kuskure, to, ina neman gafarar Allah kuma ina tuba gare shi.

Wannan kenan, kuma ina roƙon Allah Ya sanya wannan aikin nawa ya zama don neman yardarshi na yi, kuma ina roƙon shi Ya amfanar da ni da 'ya'yan Musulmi da shi, kuma Ya yafe mun abin na faɗa na kuskure da gazawa a cikinsa, lallai Shi Mai ji ne kuma Mai amsawa ne.

Daɗin tsira da aminci mai yawa ya tabbata ga Annabinmu Muhammadu, da Alayensa, da Sahabbansa, har zuwa ranar sakamako.

Rubutun:

Mabuƙaci zuwa ga yafiyar Ubangijinsa

Salahuddin bin Abdussalam Al'ubaidi

Allah Ya gafarta masa da iyayensa

**Juma'a 4 Ramadan, 1442.**

obaidisas@gmail.com 00218 91 849 1000 00966577844347

# Mataki na Farko

# 1

# Aƙida

## 1 Aƙida

## Mataki na Farko: 1

### Tambaya ta 1:

**Don me Allah Ya halicce mu?**

### Amsa: 1

**Allah Ya halicce mu ne don mu bauta Masa.**

Dalili a kan haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki:

**﴿Ban halicci Aljanu da mutane ba face don su bauta Mini﴾**

Suratuz Zariyat (56)

## Tambaya ta 2:

# Mene ne farkon wajibi a kan bayi?

## Amsa: 2

# Kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki

da dalin Hadisin Ibnu Abbas Allah Ya ƙara musu yarda, ya ce:
ya yin da Annabi ﷺ ya aika Mu'azu ɗan Jabal zuwa ga mutanen Yaman, ya ce da shi: **(Lallai kai za ka je wa wasu mutane ne ma'abota littafi, don haka ka ƙira su zuwa ga kaɗaita Allah).**

Bukhari da Muslim ne suka rawaito, kuma wannan lafazin Bukhari ne.

## Tambaya ta 3:

# Mene ne ma'anar La'ilaha illallah?

## Amsa: 3

**Ma'anarta ita ce babu abin bauta bisa cancanta sai Allah**

da dalilin faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿**Wannan kuwa saboda lallai Allah shi ne (abin bauta) na gaskiya, kuma lallai abin da suke bauta wa wanda ba Shi ba shi na ƙarya ne, kuma lallai Allah Shi ne Maɗaukaki, Mai girma**﴾. Suratul Hajji (60).

## Tambaya ta 4:

# Mene ne sharuɗan La'ilaha illallah?

## Amsa: 4

1. Ilimi
2. Yaƙini
3. Iklasi
4. Karɓa
5. Miƙa wuya
6. Gaskiya
7. So

Kamar yadda aka ɗunƙule su a baitoci guda biyu:

**Ilimi da Yaƙini da Karɓa**
**Da miƙa wiya kasan abin da nake faɗa**
**Da Gaskiya da Iklasi da So**
**Allah Ya datar da kai ga abin da yake so**

## Tambaya ta 5:

# Wane ne Ubangijinka?

## Amsa: 5

# Ubangiji na shi ne Allah

da dalilin faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai﴾.** Suratul Fatiha (2), da faɗinsa Maɗaukakin Sarki: **﴿Ka ce: "Yanzu wanin Allah zan riƙa a matsayin Ubangiji, alhali kuwa Shi ne Ubangijin komai" ﴾.** Suratul An'am (164).

## Tambaya ta 6:

# Wane ne Annabinka?

## Amsa:6

# Annabina shi ne Muhammadu (ﷺ)

da dalilin faɗin Allah Maɗaukakin Sarki:

**﴿Annabi Muhammadu bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajenku ba, sai dai (shi) ya kasance Manzon Allah ne kuma cikamakon Annabawa﴾.** Suratul Ahzab (40).

## Tambaya ta 7:

# Mene ne addininka?

## Amsa: 7

# Addinina shi ne Musulunci

da dalilin faɗinsa Maɗaukakin Sarki:

**﴾Lallai addini a wajen Allah shi ne Musulunci﴿.** Suratu Alu Imran: (19).

## Tambaya ta 8:

# A ina Allah Yake?

## Amsa: 8

# Allah Maɗaukakin Sarki Yana sama

Ya daidaita a kan Al'arshinsa, da dalilin faɗinSa Maɗaukakin Sarki:

**﴿Yanzu kun amince cewa wanda Yake sama Ya kifar da ƙasa da ku, sai kawai ku gan ta tana ta tambal-tambal﴾.**

Suratul Mulk (17),

da faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Allah Mai rahama, Ya daidaita a kan Al'arshi﴾.** Suratul Taha (4)

## Tambaya ta 9:

# Mene ne Musulunci?

## Amsa: 9

**Shi ne miƙa wuya ga Allah da kaɗaita shi, da tsayuwa gare shi wurin masa biyayya da barranta daga shirka da ma'abotanta**

dalilin haka shi ne faɗin Sa Maɗaukakin Sarki: ﴿**Sannan abin bautanku abin bauta ne guda Ɗaya, to gare Shi kawai za ku miƙa wuya. Kuma kayi albishir ga masu ƙasƙantar da kai**﴾. Suratul Hajji (34).

Tambaya ta 10:

## Nawa ne adadin rukunan Musulunci?

Amsa: 10

**Rukunan Musulunci guda biyar ne: Shaidawa lallai babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, da tsai da Salla, da ba da Zakka, da azumin watan Ramaɗana, da aikin Hajji ga wanda ya samu dama.** Dalilinsa shi ne Hadisin Ibnu Umar Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: **(an gina Musulunci a kan ginshiƙai guda biyar: Shaidawa lallai babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, da tsai da Salla, da ba da Zakka, da azumin watan Ramaɗana, da aikin Hajji ga wanda ya samu dama).** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

# 2

# Tarihin Annabi صلى الله عليه وسلم

## Tambaya ta 1:

# Mene ne sunan Annabinmu?

## Amsa: 1

**Shi ne Muhammadu ɗan Abdullahi ɗan Abdulmuɗɗalibi ɗan Hashim, shi kuma Hashim daga ƙabilar Ƙuraishawa yake, su kuma Ƙuraishawa daga Larabawa suke, Su kuma Larabawa daga Zuriyar Isma'ilu ɗan Ibrahimu- aminci Allah Ya tabbata a gare su- suke.**

## Tambaya ta 2:

# Mece ce Alkunyar Annabi ﷺ ?

## Amsa: 2

Alkunyarsa ita ce Baban Ƙasim, dalilinsa shi ne Hadisin Anas da yake cewa:

**((Wani mutum a maƙabartar Baƙi' ya yi ƙira ya ce: Ya Baban Ƙasim, sai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata gare shi ya waiwayo gare shi, sai ya ce: Ba kai nake nufi ba. Sai Annabi ﷺ ya ce: "Ku saka suna irin nawa, amma kada ku saka Alkunya irin tawa))** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## Tambaya ta 3:

# Lissafo sunayen Annabi ﷺ guda shida.

## Amsa: 3

**Sune: Muhammad, da Ahmad, da Almuƙaffi, da Alhashir, da Nabiyyur Rahma, da Nabiyyuttauba.**

Dalilinsa shi ne Hadisin Abu Musa Al'ash'ari Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce:

**((Manzon Allah ﷺ ya kasance yana ambata mana sunayensa, sai ya ce: "Ni ne Muhammad, kuma Ahmad, kuma Almuƙaffi, kuma Alhashir, kuma Nabiyyuttauba, kuma Nabiyyur Rahma)).**

Suratul An'am (164).

**Ma'anar Almuƙaffi shi ne: Al'aƙib, wato cikamakon Annabawa.**

Tambaya ta 4:

## Ga wace ƙabila Annabi ﷺ yake ɗangantuwa?

Amsa: 4

## Yana ɗangantuwa ne ga ƙabilar

# Kuraishawa

Dalilinsa shi ne Hadisin Wasila ɗan Asƙa' Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **Na ji Manzon Allah ﷺ yana cewa: (Lallai Allah Ya zaɓi Kinana daga 'ya'yan Isma'il, kuma Ya zaɓi Ƙuraish daga Kinana, ni kuma ya zaɓe ni daga Ƙuraish, kuma Ya zaɓe ni daga Banu Hashim).** Muslim ne ya rawaito.

## Tambaya ta5:

# Wace ce Mahaifiyar Annabi ﷺ ?

## Amsa: 5

**Aminatu 'yar Wahab.**

# 3

# Zikirori na Shari'a

## Tambaya ta 1:

# Me za ka ce idan ka wayi gari ko ka yini?

## Amsa: 1

An rawaito daga Abu Huraira Allah Ya ƙara masa yarda cewa: **Lallai Annabi ﷺ ya kasance yana karantar da Sahabbansa da suna cewa: (("Allahumma Bika Asbahna, wa bika amsaina, wa bika nahya, wa bika namutu, wa ilaikan-nushur".**

**idan yamma ta yi kuma ya ce: "Allahumma bika amsaina, wa bika asbahna, wa bika nahya, wa bika namutu, wa ilaikal masir)).** Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 2:

# Me za ka yi wa shimfiɗarka kafin ka kwanta bacci kuma wace addu'a za ka yi?

## Amsa: 2

Zan yi abin da Annabi ﷺ ya ba da umarnin ayi, **zan karkaɗe shimfiɗa ta da bayan bante ne, ma'ana: ɓangaren tufafi da ke taba jiki, sannan na ce: ((Bismika Rabbi, wada'atu janbi, wa bika arfa'uhu, in amsakta nafsi farhamha, wa in arsaltaha fahfazha bima tahfazu bihi ibadukassalihin))**.

**Bukhari da Muslim ne suka rawaito.**

## Tambaya ta 3:

# Me za ka ce idan za ka kwanta?

## Amsa: 3

Zan ajiye hannuna na na dama a ƙarƙashin fuskata, sannan na ce:

**"Allahumma ƙini azabaka yauma tab'asu ibadaka".**

An rawaito daga Hafsa Allah Ya ƙara mata yarda cewa: **Lallai Manzon Allah ﷺ ya kasance idan ya tashi kwanciya, yana aza hannunsa na dama a ƙarƙashin fuskarsa, sannan sai ya ce: ((Allahumma ƙini azabaka yauma tab'asu ibadaka)).** • Albani- Allah Ya jiƙan sa- ya inganta shi

## Tambaya ta 4:

# Me za ka aikata idan ka tashi yin bacci?

## Amsa: 4

**Zan tofa Ƙula'uzai da Ƙul Huwallahu a tafukan hannayena biyu.**

An rawaito daga A'isha Allah Ya ƙara mata yarda, **"lallai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance idan ya taho wajen shimfiɗarshi kowane dare, yana haɗa tafukan hannayensa biyu, sannan sai ya yi tofi a cikinsu, sai ya karanta: ((Ƙul Huwallahu Ahad)), da ((Ƙul A'uzu bi Rabbil Falaƙ)), da ((Ƙul A'uzu bi Ih Rabbin Nas)). Sannan sai ya shafi wajen da ya iya shafa da tafukan hannayensa, yana farawa da shafan kansa da fuskarsa da ɓangaren jikinsa ta gaba, kuma yana aikata haka har sau uku".** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

**Annafasu shi ne: Ɗan tattausan tofi ba tare da yawu ba.**

# Mataki na biyu

# 1

# Aƙida

## Tambaya ta 1:

# Mene ne Imani?

### Amsa: 1

Imani furuci ne da harshe, da ƙudiri a zuciya, da kuma aiki da gaɓoɓi, yana ƙaruwa da aikata ɗa'a, kuma yana raguwa da aikata saɓo, dalilin haka shi ne Hadisin Abu Huraira Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: Manzon Allah ﷺ ya ce: **((Imani yanki sabi'in da wani abu ne, ko kuma sittin da wani abu, mafi falalarsu shi ne faɗin La'ilaha illah, mafi ƙanƙantansu kuma shi ne gusar da abu mai cutarwa a kan hanya, kuma kunya yanki ne na Imani)).** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

Tambaya ta 2:

## Rukunan Imani guda nawa ne?

Amsa: 2

Rukunan imani guda shida ne, su ne: **imani da Allah, da Mala'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da ranar lahira, da imani da ƙaddara ta alheri da ta sharri. Dalilin haka shi ne Hadisin Umar ɗan Khaɗɗab Allah Ya ƙara masa yarda, cewa: ((Ka yi Imani da Allah, da Mala'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da ranar lahira, kuma ka yi imani da ƙaddara ta alheri da ta sharri)).** Muslim ne ya rawaito.

Tambaya ta 3:

# Shin imani yana ƙaruwa da raguwa?

Amsa: 3

**E, Imani yana ƙaruwa da aikata ɗa'a, kuma yana raguwa da aikata saɓo,** dalili a kan ƙaruwarsa shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Muminai na haƙiƙa su ne kaɗai waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu su raurawa, idan kuma aka karanta musu ayoyinsa, sai su ƙara musu imani, kuma ga Ubangijinsu ne suke dogaro﴾.** Suratul Anfal (2). Dalili a kan raguwarsa kuma shi ne Hadisin Abu Sa'id Alkhudri Allah Ya ƙara masa yarda, cewa: Lallai Manzon Allah ﷺ ya ce: **((Duk wanda ya ga wani mummunar aiki daga cikinku, to, ya canza shi da hannunsa, idan ba zai iya ba, to, ya canza da harshensa, idan ha kan ma ba zai iya ba, to, ya ƙi shi a zuciyarsa, kuma wannan shi ne mafi raunin imani)).** Muslim ne ya rawaito.

Tambaya ta 4:

## Mene ne mafi girman aikin nagarta?

Amsa: 4

**Shi ne kaɗaita Allah Maɗaukakin Sarki**

saboda dalilin faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Waɗanda suka yi imani, kuma ba su garwaya imaninsu da zalunci ba, waɗannan su suke da aminci, kuma su ne shiryayyu﴾.** Suratul An'am (83).

Da Hadisin Jabiru ɗan Abdullahi Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **Na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: ((Duk wanda ya haɗu da Allah baya masa shirka da wani abu, to zai shiga Aljanna, kuma duk wanda ya haɗu da Shi yana masa shirka, to, zai shiga wuta)).** Muslim ne ya rawaito

Tambaya ta 5:

## Mene ne Tauhidi?

Amsa: 5

**Tauhidi shi ne juya dukkan nau'uka na ibada ga Allah Shi kaɗai, ba tare da an Masa shirka ba.** Harwayau kuma a na cewa Tauhidi shi ne: **Kaɗaita Allah a RububiyyarSa, da UluhiyyarSa, da SunayenSa da SifofinSa.**

## Tambaya ta 6:

# Nawa ne rabe-raben Tauhidi?

## Amsa:6

**Tauhidi ya kasu kashi uku, su ne: Tauhidin Uluhiyya, da Tauhidin Rubibiyya, da kuma Tauhidin Sunaye da Sifofi.**

Dalilinsu shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Ubangijin sammai da ƙasa da kuma abin da yake tsakaninsu, sai ka bauta Masa kuma ka yi haƙuri ga bautarSa. Shin ka san wani tamkarsa﴾.** Suratu Maryam (65).

## Tambaya ta 7:

# Mene ne Tauhidin Rububiyya?

## Amsa: 7

**Shi ne Tabbatar da cewa Allah Shi kaɗai ne Mahalicci, Mamallaki, Mai jujjuya dukkan halittu gabaɗaya.**

Dalilin haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿**Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Wanda Ya halicci sammai da ƙasa, kuma Ya halicci duffai da haske; sannan waɗanda suka kafirta suna daidaita Ubangijinsu da wasu**﴾ ● Suratul An'am (1).

Tambaya ta 8:

# Mene ne Tauhidin Uluhiyya?

Amsa: 8

Shi ne juya dukkan nau'ukan bauta ga Allah Shi kaɗai ba tare da abokin tarayya ba, **Masali:** Kada mu yi sujjada ga wanin Allah kuma kada mu ƙira wani koma bayan Allah, dalilin haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿Ku bauta wa Allah, kada ku haɗa shi tarayya da wani﴾. Suratun Nisa' (36).

## Tambaya ta 9:

# Mene ne Tauhidin Sunaye da Sifofi?

## Amsa: 9

**Shi ne tabbatar da sunayen Allah da sifofinSa da aka ambace su a cikin Alƙur'ani mai girma da kuma Sunnar Annabi kamar yadda ya dace da Allah tsarki ya tabbata a gare Shi.** Dalilin haka shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Kuma Allah Yana da sunaye mafiya kyau, don haka ku roƙe Shi da su; kuma ku rabu da waɗanda suke fanɗarewa game da sunayenSa, da sannu za a yi musu sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa﴾** Suratul A'araf (180) Da faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Babu wani abu da ya yi kama da Shi; kuma Shi Mai ji ne, Mai gani﴾.** Suratul Shura (9).

## Tambaya ta 10:

# Mece ce Bauta?

## Amsa: 10

**Bauta suna ne gamamme ga dukkan abin da Allah Yake so kuma Ya yarda da shi, na furuci da ayyuka bayyanannu da ɓoyayyu, Shehin Musulunci Ibnu Taimiyya ne ya yi wannan bayani.** Dalilinsa kuma shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sariki: **﴿Ba a umurce su ba sai don su bauta wa Allah suna masu tsantsanta addini a gare shi, suna masu kauce wa ɓarna, suna kuma tsayar da salla, kuma suna ba da zakka. Wannan kuwa shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya﴾** Suratul Bayyinah (5).

# 2

# Tarihin Annabi صلى الله عليه وسلم

## Tambaya ta 1:

## Yaushe aka haifi Annabi ﷺ kuma a ina aka haifeshi?

### Amsa: 1

**An haifi Annabi tsira da amnincin Allah su tabbata a gare shi a Shekarar Giwa.** Dalilin haka shi ne Hadisin Ibnu Abbas Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **((An haifi Annabi ﷺ a Shekarar Giwa))**- Albani ya inganta shi- **kuma an haife shi ne a garin Makka.**

## Tambaya ta 2:

**Me ya sa aka sa wa wannan shekarar wannan suna?**

## Amsa: 2

**Saboda Sarki Abraha na Ƙasar Habasha ya yi ƙoƙarin rusa Ka'aba da wata runduna tare da wata giwa a wannan shekara.**

## Tambaya ta 3:

# Shin ya samu daman rusa Ka'aba?

## Amsa: 3

**A'a, bari dai, Allah Ya halakar da shi da tsuntsaye da suke jifan su da wasu duwarwatsu na wuta,**

dalilin wannan shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki:

**﴿Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya yi wa ma'abota giwa ba (1) Ashe bai mayar da makircinsu cikin watsewa ba? (2) Kuma Ya aiko da tsuntsaye dodo-dodo (3) Suna jifan su da duwatsu na ƙonanniyar laka (4) Sai da Ya mayar da su kamar karmami da aka cinye (5)﴾.** Suratul Fil

## Tambaya ta 4:

**Wane ne ya raini Annabi ﷺ ?**

## Amsa: 4

**Shi ne kakansa Abdulmuɗɗalib, sannan sai baffansa Abu Ɗalib.**

## Tambaya ta 5:

# Mene ne halayyar Annabi ﷺ ?

## Amsa: 5

# Halayyarsa su ne abin da Alƙur'ani ya zo da shi

dalilin haka shi ne Hadisin Sa'ad ɗan Hashim ɗan Amir Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: Na ce: **Ya Uwar Muminai! Ki sanar da ni halayyar Annabi ﷺ mana. Sai ta ce:** **((Ba kana karanta Alƙur'ani ba. Na ce mata: E, sai ta ce: to, halayyar Annabi ﷺ su ne Alƙur'ani)).** **Muslim ne ya rawaito.**

## Tambaya ta 6:

## A ina Annabi ﷺ ya kasance yana bauta a farkon lamarinsa?

## Amsa: 6

**Ya kasance yana bauta ne a kogon Hira'**, dalilin haka shi ne Hadisin A'isha Allah Ya ƙara mata yarda, ta ce: **((Lallai Annabi ﷺ ya kasance yana keɓantuwa a kogon Hira', sai yana bauta wa Allah na wasu darare ƙididdigaggu)).** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## Tambaya ta 7:

# Yaushe wahayi ya fara sauƙo wa Annabi ﷺ ?

## Amsa: 7

**Wahayi ya fara sauƙo masa ne lokacin da ya kai shekara arba'in**

**(40) a duniya**

dalilin haka shi ne Hadisin Anas ɗan Malik, ya ce: **((Allah Ya aiko shi lokacin da ya cika shekara arba'in)).**

# 3

# Zikirori na Shari'a

## Tambaya ta1:

# Akwai wata aya mai girma da muke karanta ta kafin muyi bacci, mece ce wannar ayar?

## Amsa: 1

Ita ce **Ayatul ƙursiyyu**, wato faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Allahu la'ilaha illa huwal hayyulƙayyun, la ta'khuzuhu sinatun wala naum, lahu ma fissamawati wa ma fil'ard, man zallazi yashfa'u indahu illa bi'iznih, ya'lamu ma baina aidihim wama khalfahum, wala yuhiɗuna ba shai'in min ilmihi illa bima sha', wasi'a kursiyyuhus-samawati wal ard, wala ya'uduhu hifzuhuma, wa huwal aliyyul azim﴾.** Suratul Baƙara (255).

An rawaito daga Abu Hurairara Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **((Manzon Allah ﷺ ya sa ni gadin Zakkar Ramaɗan, sai wani mutun ya zo mun, sai ya riƙa ɗiba daga wannan abincin, sai na kama shi, sai na ce: wallahi sai na kai ka wajen Manzon Allah ﷺ. Sai ya Ambato Hadisin, sai ya ce: "Idan ka koma zuwa shimfiɗarka lokacin bacci, to, ka karanta Ayatul Kursiyyu, idan ka yi haka; ba za ka gushe ba tare da wani mai baka kariya da Allah Zai turo maka, kuma Shaiɗan ba zai kusance ka ba har ka wayi gari". Sai Annabi ﷺ ya ce: "Gaskiya ya faɗa maka, amma shi ɗin maƙaryaci ne")).** Bukhari ne ya rawaito.

Tambaya ta 2:

## Akwai wasu ayoyi guda biyu a ƙarshen wata sura da ake karantawa lokacin bacci, Waɗanne ayoyi ne su?

Amsa: 2

Sune **ayoyi biyu na ƙarshen suratul Baƙara**: **﴿Amanar-rasulu bima unzila ilaihi min rabbihi wal-mu'minuna kullun amana billahi wa mala'ikatihi wa kutubihi wa rusulih, la nufarriƙu baina ahadin min rusulih, wa ƙalu sami'na wa aɗa'na gufranaka rabbana wa ilayka-masīr (285) La yukallifullahu nafsan illa wus'aha, laha ma kasabat wa 'alayha maktasabat, rabbana la tu'akhizna in nasina au akhɗa'na, rabbana wa la tahmil 'alaina isran kama hamaltahu alallazina min ƙablina, rabbana wa la tuhammilna ma la ɗaƙata lana bih, wa'fu 'anna wagfir lana warhamna, anta mawlana fan-surnaa alal-ƙaumil-kafirin﴾**. Suratul Baƙara (286).

An karɓo daga Abu Sa'id Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: Annabi ﷺ ya ce: **((Duk wanda ya karanta ayoyi guda biyu na ƙarshen suratul Baƙara da dare, to, sun isar masa)).** Bukhari ne ya rawaito.

**Ma'anar sun isar masa, wato sun isar masa daga masifu a wannan daren. Wasu kuma suka ce: Sun isar masa tsayuwar dare.**

**Tambaya ta 3:**

**Akwai wata sura da muke karanta ta kafin bacci saboda nuna barrantarmu daga shirka, wace sura ce?**

**Amsa: 3**

ita ce: **Suratul ƙafirun**:

**﴿Ƙul ya ayyuhal-kafirun (1) La a'budu ma ta'budun (2) Wa la antum 'abiduna ma a'bud (3) Wa la ana 'abidun ma abadtum (4) Wa la antum 'abiduna ma a'bud (5) Lakum dinukum waliya din (6) ﴾.**

An rawaito daga Naufal Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: Manzon Allah ﷺ ya ce da ni: **((ka karanta (Ƙul ya ayyuhal-kafirun), sannan sai ka yi bacci da zaran ka kammala karantawa, lallai ita barranta ce daga shirka)).** Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 4:

**Akwai wani zikiri da ake yi kafin bacci, kuma Annabi ﷺ ya ce game da wannan zikirin: "Ya fi alheri a kan hadimi) Wane zikiri ne wannan?**

## Amsa: 4

shi ne faɗin: **"Subhanallahi' sau talatin da uku (33), "Alhamdu lillahi" sau talatin da uku (33), da kuma "Allahu Akbar", shi ma sau talatin da uku (33)**. An rawaito daga Aliyyu Allah Ya ƙara masa yarda cewa: **Lallai Faɗimatu Allah Ya ƙara mata yarda ta je wajen Annabi ﷺ tana neman ya bata hadimi, sai ya ce: ((Ashe ba zan baki labarin abin da ya fi wannan alheri ba? Ki ce: "Subhanallahi' sau talatin da uku (33) idan ki ka tashi yin bacci, "Alhamdu lillahi" sau talatin da uku (33), da kuma "Allahu Akbar" shi ma sau talatin da uku (33). Ya ce: tun daga wannan lokacin ban taɓa barin su ba)).** **Bukhari ne ya rawaito.**

## Tambaya ta 5:

# Me za ka ce idan za ka shiga bayan gida?

## Amsa: 5

**Zan ce: "Bismillahi"**

**Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Shamaki da ke tsa kanin aljanu da al'aurar mutane shi ne idan mutun zai shiga bayan gida ya ce: "Bismillahi")).** Albani - Allah Ya jiƙanshi - ya inganta shi.

Sannan sai na ce: **((Allahumma inni A'uzu bika minal khubusi wal khaba'isi)).**
Bukhari ne ya rawaito

## Tambaya ta 6:

# Me za ka ce idan za ka ci abinci ko za ka sha abin sha?

## Amsa: 6

Zan ce: **"Bismillahi".**

**Annabi ﷺ ya ce: ((Idan ɗayanku zai ci abinci, to, ya ce: "Bismillahi", idan kuma ya mance a farko, to, idan (ya tuna) ya ce: "Bismillahi Auwalahu wa akhirahu)).**

Albani Allah Ya jiƙanshi ya inganta shi.

# Mataki na Uku

# 1

# Aƙida

## Tambaya ta 1:

# Mene ne Alkur'ani?

## Amsa:1

Shi **Maganar Allah ne**, **kuma ba halitta ba ne**, dalilin haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Idan wani daga cikin mushirikai ya nemi taimakonka, ka ba shi taimako har ya ji Maganar Allah﴾**. Suratul Taubah (6).

## Tambaya ta 2:

# Mene ne mafi girman laifi?

## Amsa:2

**Shi ne** **shirka ga Allah Maɗaukakin Sarki,** dalili shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Lallai Allah ba ya gafarta a yi Masa shirka, amma kuma yana gafarta koma bayan haka ga wanda ya ga dama﴾.** Suratun Nisa' (48). An rawaito daga Abdullah ɗan Mas'ud Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **Na tambayi Manzon Allah ﷺ: Wane zunubi ne mafi girma? Sai ya ce:** **((Ka sanya wa Allah abokin tarayya alhali shi ne ya halicce ka)).** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## Tambaya ta 3:

# Mene ne Shirka?

## Amsa:3

Shi ne **hada wanin Allah tare da Allah a cikin bauta**

An rawaito daga Abu Huraira Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **Manzon Allah ﷺ ya ce: "Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ((Ni ne nafi ababen tarayya wadatuwa daga shirka, duk wanda ya aikata wani aiki da ya yi shirka da ni tare wanda ba ni ba a cikinsa, to, zan ƙyale shi da shirkarsa)).**

**Muslim ne ya rawaito.**

## Tambaya ta 4:

# Shin aiki zai yi amfani tare da shirka?

## Amsa:4

**Ba zai amfanar ba, saboda shirka tana lalata aiki**

dalili shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿Kuma da a ce sun yi shirka, to, da lallai duk abin da suka kasance suna aikatawa ya rushe﴾.** Suratul An'am (89).

## Tambaya ta 5:

**Mene ne abin da Manzanni gabaɗaya suka yi ƙira a kai?**

## Amsa:5

**Shi ne bauta wa Allah shi kaɗai, da kafirce wa Ɗagutu**

dalili shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴾Haƙiƙa kuma Mun aiko Manzo a kowacce al'umma cewa: "Ku bauta wa Allah, kuma ku nisanci Ɗagutu" ﴿.**

Suratun Nahl (36).

### Tambaya ta 6:

## Mene ne kafirci?

### Amsa:6

**Shi ne: Duk abin da ke kishiyantar Imani, daga kuduri, ko furuci, ko aiki**

Allah Madaukakin Sarki Ya ce:

**﴾Duk kuwa wanda ya kafirce wa Imani, hakika aikinsa ya rushe, kuma a ranar lahira yana cikin asararru﴿.** Suratul Ma'ida (6).

## Tambaya ta 7:

# Mene ne hukuncin kiran mamata da neman agajinsu?

## Amsa:7

**Hakan shirka ne babba, mai cire mutum daga addini**

dalili shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: ﴿**Wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amsa ma sa ba har zuwa ranar alƙiyama, kuma su (ababen bautar) rafkanannu ne game da bautar da suke yi musu (5) Idan kuma aka tashi mutane (ababen bautar za su kasance abokan gabarsu kuma su zamo masu musanta bautar tasu**﴾. Suratul Ahqaf(5-6). An rawaito daga Ibnu Mas'ud Allah Ya ƙara masa yarda**Duk wanda ya mutu alhali yana kiran wani koma bayan Allah zai shiga wuta))**. Bukhari ne ya rawaito.

## Tambaya ta 8:

# Me ka sani game da bidi'a?

## Amsa:8

**Bidi'a** ita ce: **Bauta da abin da Allah da ManzonSa ba su shar'anta ba.**

Manzon Allah ﷺ ya ce: **((Duk wanda ya ƙirƙri wani abu cikin wannan lamari namu da baya cikinsa, to, an mayar masa)).** Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## Tambaya ta 9:

# Mene ne hukuncin bidi'a tare da kawo misalinta?

## Amsa:9

Bidi'ah haramun ce kuma ɓata ce bayyananniya, kuma laifi ne mai girma, Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Duk wanda ya ƙirƙri wani abu cikin wannan lamari namu da baya cikinsa, to, an mayar masa)). Bukhari da Muslim ne suka rawaito. Ma'anar an mayar masa, wato: an mayar wa ma'abocinsa.

Misalan bidi'a:

- Bidi'ar furta niyyar Salla da Alwala,
- Bidi'ar zikirin jama'a tare bayan idar da Salla, bidi'ar bikin haifuwar Annabi ﷺ da hijirarsa
- Bidi'ar bikin daren Isra'i da Mi'raji.

Tambaya ta 10:

## Mene ne hatsarin bidi'a?

Amsa:10

Hatsarin bidi'a shi ne abubuwa masu zuwa:

- Cewa lallai ana mayar da aikin ɗan bidi'a gare shi, Allah ba ya karɓa ko da kuwa ma'abocinta yana da kyakkyawar niyya.

- Cewa lallai bidi'a tana rusa Hadisai ingantattu kuma tana rage yaɗuwarsu.

- Cewa lallai ɗan bidi'a ana hana shi tuzgar tafkin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata gare shi.

Mataki na Uku: 3

# 2

# Tarihin Annabi صلى الله عليه وسلم

## Tambaya ta 1:

# Me kafiran Ƙuraishawa suke kiran Annabi ﷺ kafin aiko shi?

## Amsa: 1

# suna kiran shi ne da mai gaskiya amintacce

dalili shi ne Hadisin Ummu salma Allah Ya ƙara mata yarda a labarin hijira zuwa Habasha, da tambayar da Annajjashi ya yi wa Ja'far ɗan Abu Ɗalib, **cikin labarin akwai cewa: ((Har zuwa lokacin da Allah Ya aiko mana wani Manzo daga cikinmu, wanda mun san nasabarsa, da gaskiyarsa, da amanarsa, da kamun kai)).** Muslim ne ya rawaito.

## Tambaya ta 2:

**wane ne ya yi Imani da Annabi ﷺ kuma ya ce da shi: "Lallai babu wani da ya taɓa zuwa da irin abin da ka zo da shi face sai an yi ƙiyayya da shi?**

## Amsa: 2

Shi ne **Waraƙatu ɗan Naufal**

dalili shi ne Hadisin A'isha Allah Ya ƙara mata yarda, ta ce: **(( Waraƙatu ɗan Naufal, kuma shi ya kasance kirista ne, kuma yana karanta Littafin Injila da yaren Larabci....))** ▪ Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## Tambaya ta 3:

# Me aka zana a kan zoben Annabi ﷺ?

## Amsa: 3

**An yi zoben nashi ne da azurfa, kuma an zana Muhammadun Rasulullah a kai, kowace kalma a layi daban**

dalili shi ne Hadisin Anas cewa: ((lallai Abubakar Allah Ya ƙara masa yarda yayin da ya zama Halifa ya aika shi zuwa garin Bahrain, kuma ya rubuta masa wannan takarda, kuma ya yi masa hatama da zoben Annabi ﷺ, kuma zanen wannan zoben ya kasance a layi uku ne, **(Muhammad) a layi daban, (Rasul) a layi daban, (Allah) a layi daban)).**

ukhari da Muslim ne suka rawairo.

## Tambaya ta 4:

# Ambaci sunayen Matan Annabi ﷺ ?

## Amsa: 4

**Matan Annabi ﷺ sune:**

**1. Khadija ‘yar Khuwailin 2. Zainab ‘yar Khuzaima.**

**Wađannan biyun sun riga Annabi ﷺ rasuwa.**

**3. Saudatu ‘yar Zam’a**

**4. Zainabu ‘yar Jahash**

**5. Aisha ‘yar Abubakar Siddiƙ**

**6. Maimunatu ‘yar Alharis**

**7. Hafsatu ‘yar Umar**

**8. Ramlatu ‘yar Abu Sufyan**

**9. Hindu ‘yar Abu Umayya**

**10. Safiyyatu ‘yar Huyayyu**

**11. Juwairiyya ‘yar Alharis.**

Dalili shi ne Hadisin da Ađa’u ya rawaito, ya ce: “Mun halarci jana’izar Maimuna matar Annabi (SAW), tare da Ibnu Abbas a wani waje da ake ce wa Sarifa, sai Ibnu Abbas ya ce: Wannan matar Annabi ﷺ ce, don haka idan kuka đaga makararta, kada ku girgiza ta, kuma kada ku jijjiga ta, ku bi a hankali, saboda lallai Manzon Allah ﷺ ya kasance yana da mata tara, ya kasance yana rabon kwana ga guda takwas, amma ba ya rabawa da guda đaya cikinsu”. Wađannan mata taran kuma, su ne wađanda Annabi ﷺ ya rasu alhali suna ƙarƙashinsa.

## Tambaya ta 5:

# ‘ya’yan Annabi ﷺ guda nawa ne? kuma mene ne sunayensu?

## Amsa: 5

**‘ya’yan Annabi ﷺ maza da mata - Allah Ya ƙara musu yarda - dukkansu ‘ya’yan matarsa uwar Muminai Khadija ne, Allah Ya ƙara mata yarda, sai Ibrahim kaɗai, shi ɗan kuyangar Annabi Mariya ne, Allah Ya ƙara mata yarda, wacce Almuƙauƙis sarkin Iskandariyya kuma shugaban ƙibɗawa ya ba shi.**

**Kuma ‘ya’yan Annabi ﷺ a bisa magana mafi inganci su bakwai ne, uku maza huɗu mata.**

Mazan su ne: **Alƙasim, Abdullahi, da Ibrahim.**

Matan kuma su ne: **Zainab, Ruƙayya, Ummu Kulsum, da Fadima.**

**Kuma dukkan ‘ya’yansa sun riga shi rasuwa, sai Fadima Allah Ya ƙara mata yarda kaɗai, ita ta rasu ne bayan rasuwarsa.**

# 3

# Zikirori na Shari'a

## Tambaya ta 1:

# Me za ka ce idan ka gama cin abinci ko shan abin sha?

## Amsa: 1

**Zan ce: "Alhamdu lillahi".**

Annabi tsira da aminci Allah su tabbata a gare shi ya ce: **((Duk wanda ya ci abinci, sannan ya ce: "Alhamdu lillahil lazi Aɗ'amani haza, wa razaƙanihi min gairi haulin minni wala ƙuwwatin". Za a gafarta masa abin da ya gabata na zunubansa)).**

Albani - Allah Ya jiƙansa - ya inganta shi.

## Tambaya ta 2:

# Me za ka ce idan zaka fita daga gida?

## Amsa: 2

Zan ce: **"Bismillahi tawakkaltu alallahi, wala haula wala ƙuwwata illa billahi".**

**Idan mutum ya faɗi hakan, za a ce da shi a wannan lokacin "an isar maka kuma an kare ka", sai Shaidan ya yi nesa da shi.**

Albani ya ce Hadisi ne Hasan.

## Tambaya ta 3:

# Me za ka ce idan ka je duba mara lafiya?

## Amsa: 3

An rawaito daga Ibnu Abbas Allah Ya ƙara masa yarda, cewa: **lallai Annabi ﷺ ya kasance idan ya shiga duba mara lafiya yana cewa: "la ba'sa ɗahurun in sha Allah".**

**Bukhari da Muslim ne suka rawaito.**

## Tambaya ta 4:

# Mene ne Sayyidul Istigifari?

## Amsa: 4

An rawaito daga Shaddad ɗan Aus Allah Ya ƙara masa yarda, daga Annabi ﷺ ya ce: **((Siyyidul Istigifari shi ne ka ce:** **"Allahumma anta rabbi, la ilaha illa anta, khalaƙtani wa ana abduka wa ana ala ahdika wa wa'dika mastaɗa'tu a'uzu bi-ka min sharri ma sana'tu, abu'u laka bi-ni'matika 'alayya wa abuu' bi-zanbi faghfir li fa'innahu la yaghfiruz-zunuba illa anta".** **Wanda ya faɗe ta da rana alhali yana mai yaƙini da ita, sai ya mutu kafin yamma, to, yana cikin 'yan aljanna, duk wanda kuma ya faɗe ta da daddare alhali yana mai yaƙini da ita, sai ya mutu kafin safiya, to, shi ma ɗan aljanna ne)).** Bukhari ne ya rawaito.

## Tambaya ta 5:

# Me za ka ce idan ka ga abin da ya birge ka?

## Amsa: 5

Zan ce: **"Barakallahu fihi Allahumma barik fihi".**

**Dalili shi ne faɗin Manzon Allah ﷺ: ((Idan ɗayanku ya ga wani abu da ya birge shi tare da ɗanuwansa, ko a kansa, ko a dukiyarsa, to, ya roƙi Allah Ya sanya masa albartka, saboda kambun baka gaskiya ne)).** Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 6:

# Me zaka ce idan zaka sanya sabon tufafi?

## Amsa: 6

An rawaito daga Abu Sa'id Alkhudri Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: **Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance idan ya yi sabon kaya; sai ya ambace shi da sunanshi, riga ce ko kuma rawani ne, sannan ya ce: ((Allahumma lakalhamdu, Anta kasautanihi, As'aluka min khairihi wa khairi ma suni'a lahu, wa a'uzu bika min sharrihi wa sharri ma suni'a lahu)).** Albani ya inganta shi.

# Mataki na huɗu

Mataki na huɗu: 4

# 1

# Aƙida

1 **Aƙida**

**Mataki na huɗu: 4**

**Tambaya ta 1:**

## Mene ne addinin da Allah ba ya karɓar waninsa?

**Amsa: 1**

**Shi ne Musulunci,**

dalili shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: ﴿**Duk kuma wanda ya nemi (bin) wani addini ba Musulunci ba, to, har abada ba za a karɓa daga gare shi ba, kuma shi a lahira yana cikin hasararru**﴾. Suratu Alu Imran (84).

## Tambaya ta 2:

# Mene ne sharuɗaun La'ilaha illah?

## Amsa: 2

**Su ne kamar haka:**

**1. Ilimi:** Da dalilin faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿To, ka sani cewa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma ka nemi gafarar zunubanka﴾.** Suratu Muhammad (19).

**2. Yaƙini:** Dilili shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Muminai kawai su ne waɗanda suka yi imani da Allah da ManzonSa, sannan ba su yi kokonto ba﴾.** Suratul Hujurat (15).

**3. Miƙa wuya:** Dalilinsa shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Wanda kuma ya miƙa kansa ga Allah, yana kuma mai kyautatawa, to, haƙiƙa ya yi riƙo da igiya ƙwaƙƙwara. Kuma ƙarshen al'amura zuwa ga Allah ne﴾.** Suratu Luƙman (22).

**4. Karɓa:** Dalilinsa shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki game da lamarin waɗanda suka ƙi karɓanta: **﴿Lallai su sun kasance idan aka ce da su babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, sai su yi girman kai﴾.** Suratus-Saa'fat (22).

**5. Tsantsanta niyya ga Allah:** Dalilinsa shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Ku saurara! Tsantsan addini na Allah ne﴾.** Suratuz-Zumar (3).

**6. Gaskiya:** Dalilinsa shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Haƙiƙa kuwa mun jarrabi waɗanda suke gabaninku; to tabbas kuwa Allah zai bayyana waɗanda suka yi gaskiya, lallai kuma zai bayyana maƙaryata﴾.** Suratul Ankabut (3).

**7. So:** Dalilinsa shi ne faɗinSa Maɗaukakin Sarki: **﴿Ya ku waɗanda suka yi imani, duk wanda ya yi ridda daga cikinku, ya bar addininsa, to (ya sani) Allah zai kawo waɗansu mutane da Yake son su suke son Sa﴾.** Suratul Ma'ida (54).

**Kamar yadda aka ɗunƙulesu a baitoci guda biyu:**

**Ilimi da Yaƙini da Karɓa**
**Da miƙa wiya kasan abin da nake faɗa**
**Da Gaskiya da Iklasi da So**
**Allah Ya datar da kai ga abin da yake so**

1 **Aƙida**

**Mataki na huɗu: 4**

**Tambaya ta 3:**

# Mene ne sharuɗan karɓar bauta?

**Amsa: 3**

**Sune kamar haka:**

**1. Tsantsanta niyya ga Allah Maɗaukakin Sarki.**

**2. Koyi da Manzo** ﷺ, dalili a kan haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿**Ba'a umurce su ba face su bauta wa Allah, suna masu kadaita addini a gare shi, suna masu karkace wa ɓata), su tsayar da sallah, su bada zakka, wannan shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya**﴾. Suratul Bayyinah (5). An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: **Manzon Allah** ﷺ **ya ce:** Allah Ya ce: **((Na wadata daga Abokan tarayya a kan shirka, duk wanda ya yi aiki ya haɗani da wani cikinsa, zan kyaleshi da shirkarsa)** Muslim ne ya ruwaito. An karɓo daga A'isha (RA) ta ce: Manzon Allah ﷺ ya ce: **((duk wanda ya aikata aiki da babu umurninmu a kansa, to za'a mayar masa)).** Muslim ne ya ruwaito

## Tambaya ta 4:

# Mene ne mas'aloli guda hudu da ya zama wajibi a kanmu mu san su?

## Amsa: 4

**Na farko: Ilimi.**

**Na biyu: Aiki da shi.**

**Na uku: Kira izuwa gare shi.**

**Na hudu: Huƙuri da cutarwa dake cikinsa.**

Dalili a kan haka faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿**Ka sani Lallai babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, ka nemi gafarar zunubinka, da na mumunai maza, da mumunai mata, Allah Ya san kai-kawonku da makomarku**﴾. Suratu Muhammad (19).

Da faɗinSa Maɗaukaki: ﴿**Na rantse da lokaci (1) Lallai mutum yana ciki hasara (2) Sai dai waɗanda suka yi Imani kuma suka yi ayyuka nagari, kuma suka yi wasici da gaskiya kuma suka yi wasici da hakuri**﴾. Suratul Al-asr (3-1).

### Tambaya ta 5:

## Mene ne tushe guda uku da ya zama wajibi a kan Musulmi ya san su?

### Amsa: 5

**Bawa ya san Ubangijinsa, ya san addinin Musulunci da dalilai, kuma sune tambayoyi guda uku da ake tambayar mutum a cikin ƙabarinsa,** dalili a kan haka, Hadisin Albara'u ɗan Azib mai tsawo, a cikinsa Annabi ﷺ ya ce: **((Sai Mala'iku guda biyu su zo masa, sai su zaunar da shi, sai su ce da shi: Wane ne Ubangijinka? sai ya ce: Ubangijina shi ne Allah, sai su ce da shi: Mene ne addininka? Sai Ya ce: Addinina shi ne Musulunci, sai su ce da shi: Me za ka ce game da mutumin nan da aka aiko shi a cikinku, sai ya ce: Shi Manzon Allah ne ﷺ)).** Imam Ahmad ya ruwaito shi a cikin Musnad, Albani kuma ya inganta shi Allah Ya yi masa rahma.

1 Aƙida

Mataki na huɗu: 4

Tambaya ta 6:

## mene ne muhimmancin Addu'a?

Amsa: 6

## Addu'a ita ce ibada

an karɓo daga Nu'uman ɗan Bashir, ya ce: **Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Addua ita ce ibada))**

**Albani ya Inganta shi.**

## Tambaya ta 7:

### A kan wane tafarki ake haifan yaro?

## Amsa: 7

### A kan tafarkin Musulunci

dalili a kan haka shi ne Hadisin Abu Huraira رضي الله عنه, ya ce: **Manzon Allah** ﷺ **ya ce: ((Ana haifan kowane yaro ne a kan tafarkin musulunci, iyayensa su za su Yahuɗantar da shi, ko su Kiristantar da shi, ko su Maguzantar da shi))**

Bukhari da Muslim ne su ka ruwaito.

## Tambaya ta 8:

# cikin mutane wane ne ya fi soyuwa a wurin Allah, Mumini mai rauni ko mumini mai ƙarfi?

## Amsa: 8

Mumini mai ƙarfi ya fi soyuwa a wurin Allah, dalili a kan haka Hadisin Abu Huraira (رضي الله عنه), ya ce: **Manzon Allah (صلى الله عليه وسلم) ya ce:** **((Mumini mai ƙarfi ya fi soyuwa a wurin Allah a kan Mumini mai rauni, amma cikin kowannensu akwai alheri, yi kokari wurin abin da zai amfane ka, ka nemi taimakon Allah kada ka gajiya, idan wani abu ya same ka, kada ka ce: Da na aikata abu kaza, zai kasance kaza da kaza, sai dai ka ce: Allah shi ya ƙaddara, abin da ya so shi yake faruwa, saboda (da na sani) tana buɗe kofar Shaiɗan))**. ■ Muslim ne ya ruwaito.

## Tambaya ta 9:

# Mene ne mafi girman laifi?

## Amsa: 9

**Shirka da Allah, da kuma ƙuntatawa iyaye, da shaida ta ƙarya.**

An karɓo daga Abu Bakrata Nufai'u ɗan Alharis, ya ce: **((Annabi) Bai gushe ba yana maimaitawa har sai da muka ce inama a ce ya dakata haka))** bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

## Tambaya ta 10:

### Su waye ne waliyyan Allah?

## Amsa: 10

**Su ne waɗanda suka yi imani, sannan suka kasance masu kiyaye dokokin Allah**

dalili a kan haka shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ﴿**Ku saurara! Lallai waliyyan Allah babu tsoro a tare da su, kuma ba su da baƙin ciki (62) Sune waɗanda suka yi imani kuma suka kasance masu kiyaye dokokin Allah**﴾. Suratu Yunus (63-62).

Mataki na huɗu: 4

# 2

# Tarihin Annabi ﷺ

## Tambaya ta 1:

# Wane ne sarkin Habasha da ya ba wa sahabbai mafaka, ya kuma ba su kariya?

## Amsa: 1

## Annajjashi Allah Ya masa rahma

Dalili a kan haka Hadisin Ummu-salama رضي الله عنها game da ƙissar hijira zuwa Habasha, ya zo a cikinta cewa: **((yayin da muka isa ƙasar Habasha, mun sauka a wurin mafi alherin mai ba da kariya, wato Annajashi, ya amintar da mu a kan addininmu, muka bauta wa Allah babu cutarwa, kuma ba mu ji wani abin ƙi ba)).** Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 2:

# Mene ne Annabi ﷺ ya aikata yayin rasuwar Annajashi Allah Ya yi masa rahama?

## Amsa: 2

## Ya sanar da mutuwarsa

kuma ya yi masa sallah ta ga'ibi **((Wato wanda ba ya nan))**, dalili a kan haka Hadisin Abu huraira رضي الله عنه ya ce: **Lallai Manzon Allah ﷺ ya sanar da mutuwar Annajashi a ranar mutuwarsa, kuma ya fita izuwa wurin salla, sai ya yi sahu da su, ya yi kabbarori guda hudu))**. Bukhari ne ya ruwaito.

## Tambaya ta 3:

# Shekara nawa Annabi ﷺ ya yi a Makkah kafin hijra?

## Amsa:3

# Ya yi shekara goma sha uku

dalili a kan haka Hadisin Abdullahi ɗan Abbas Ya ce: **(An yi wa Manzo ﷺ wahayi yana ɗan shekara arba'in, ya zauna a Makka tsawon shekara goma sha uku, sai aka umurce shi da hijra, ya yi hijira izuwa Madina ya zauna a cikinta tsawon shekara goma, sannan ya yi wafati ﷺ**.

**Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.**

## Tambaya ta 4:

# Wani wuri Annabi ﷺ ya riƙa saboda da'awa a farkon al'amarinsa?

## Amsa: 4

**Gidan Arƙam ɗan Abul Arƙam**

## Tambaya ta 5:

# Wane ne farkon wanda ya musulunta tare da Annabi ﷺ?

## Amsa: 5

**Daga cikin mazaje:**

**Abubakar siddiƙ رضي الله عنه,**

**a cikin yara kuwa:**

**Aliyu ɗan Abu Ɗalib رضي الله عنه,**

**a cikin mata kuma:**

**Khadija 'yar Khuwailid رضي الله عنها.**

Muhammad ɗan Ka'ab ya ce: **((Lallai mutum na farko da ya musulunta a cikin wannan Al'umma tare da Annabi ﷺ: Khadija, mazajen farko guda biyu da suka musulunta kuwa su ne: Abubukar da Aliyu, kuma lallai Abubakar shi ne mutum na farko da ya fara bayyana Musuluncinsa)).** Imamu Ahmad ya ruwaito, a littafin falalar sahabbai.

Tambaya ta 6:

## Izuwa ina aka yi isra'i (tafiyar dare) da Annabi ﷺ?

Amsa: 6

# Izuwa Masallacin Ƙudus

Dalili a kan haka shi ne faɗin Allah Maɗaukaki: **﴿Tsarki ya tabbata ga (Allah) Wanda Ya yi isra'i da bawansa cikin dare, daga Masallaci mai alfarma zuwa Masallaci mai nisa wanda muka albarkaci ilahirinsa, saboda mu nuna masa ayoyinmu, lallai fa Shi Mai ji ne kuma Mai gani ne﴾.** Suratul Isra (1).

## Tambaya ta 7:

**Izuwa ina aka yi mi'iraji (hawa sama) da Annabi ﷺ?**

## Amsa: 7

**An yi mi'iraji da shi izuwa sama**

## Tambaya ta 8:

# Mene ne sunan dabbar da aka yi isra'i da shi a kanta?

## Amsa: 8

# Sunanta Buraƙ

Dalili a kan haka Hadisin Anas ɗan Malik رضي الله عنه, **ya ce: Annabi ﷺ ya ce: ((Sai aka zo mun da dabba fara, ba ta kai alfadari ba amma ta fi jaki, a na kiran ta Buraƙ, sai na tafi tare da Jibrilu har muka kawo saman duniya)).**

**Imamu Muslim ne ya ruwaito.**

Mataki na hudu: 4

# 3

# Zikirori na Shari'a

**Tambaya ta 1:**

## Me za ka ce idan wani abu ya same ka, ko kuma ya tsananta a gare ka?

**Amsa: 1**

**Zan ce: ((La'ilaaha Illallahul Azeemul haleem, La'ilaaha Illallahu Rabbul Arshil azeem, La'ilaha Illallahu Rabbus samawati wa Rabbul Ardi Rabbul arshil kareem)).** An karɓo daga ɗan Abbas (RA): Lallai Annabi (SAW) ya kasance idan wani al'amari ya tsananta gare shi yana cewa: **((La'ilaaha Illallahul Azeemul haleem, La'ilaaha Illallahu Rabbul Arshil azeem, La'ilaha Illallahu Rabbus samawati wa Rabbul Ardi Rabbul arshil kareem)).** Bukhari da Muslim ne suka ruwaito, kuma wannan lafazin Muslim ne.

Tambaya ta 2:

## Me za ka ce lokacin kallon jinjirin wata?

Amsa: 2

**Zan ce:** **((Allahumma ahillahu alaina bil amni wal imani, was-salamati wal islaami wattaufeeƙi lima tuhibbu wa tardha, Rabbuna wa Rabbukallah)).**
An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar رضي الله عنه, Manzon Allah ﷺ ya kasance idan yaga jinjirin wata yana cewa: **((Allahumma Ahillahu Alaina Bil Amni wal Iymani, wassalamati wal islaami wattaufeeƙi lima tuhibbu wa tardha, Rabbuna wa Rabbukallah)).** Albani ya inganta shi.

**Tambaya ta 3:**

## Wace sura ce  aka sunnanta karanta ta a ranar Juma'a, kuma shin tana da lokaci kayyadadde?

**Amsa: 3**

Ita ce **Suratul-kahafi**

**Lokacinta shi ne:**

**Daga fitowar Alfijir na ranar Juma'a har zuwa faduwar rana.**

## Tambaya ta 4:

# Me za ka faɗawa iyalanka idan za ka yi tafiya?

## Amsa: 4

**Zan ce da su: "Astaudi'ukumullaha Allazi laa tadi'u wada'i'uhu"**

an rawaito daga Abu huraira Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: Manzon Allah ﷺ ya kira ni, **sai ya ce da ni: ((Astaudi'ukallaha Allazi laa tadee'u wada'i'uhu)).** Albani ya inganta shi, **Mazauni kuma zai ce wa matafiyi "Astaudi'ukallaha dinaka wa ama'nataka wa khawatima amalika".** An karɓo daga Salim yana cewa: Ibnu Umar رضي الله عنه yana ce wa mutum idan ya yi niyyar tafiya **(Matso kusa da ni na maka bankwana kamar yadda Annabi ﷺ yake mana bankwana, sai ya ce: (Astaudi'ullaha dinaka wa amanataka wa khawateema amalika).** Albani ya inganta shi

## Tambaya ta 5:

# Me za ka ce idan ka hau abin hawa a halin tafiya?

## Amsa: 5

Zan ce: "Allahu akbar sau uku, Subhanallazi sakhkhara lana haza wama kunna lahu muƙrinina, wa Inna ila Rabbina Lamunƙalibuna, Allahumma inna nas'aluka fi safarina haza Albirra wat-taƙwa, wa minal amali ma tardha, Allahumma hawwin alaina safarana haza, waɗwi anna bu'dahu, Allahumma antas-sahibu fis-safar, wal khalifatu fil-ahli, Allahumma inni a'uzu bika min wa'sa'is-safar, wa kaa'batil manzari, wa su'il manƙalabi fil ma'li wal-ahli wal-walad, idan ka dawo sai ka faɗe su kuma ka ƙara da cewa: Ayibuna, Ta'ibuna, Abiduna Lirabbina Hamiduna". Muslim ne ya ruwaito.

Tambaya ta 6:

## Mene ne matifiyi zai faɗa idan ya ga wata alƙariya ko gari da ya nufaci shiga cikinsu?

Amsa: 6

Zan ce: **"Allahumma Rabbas samawati wama azlalna, wa Rabbal aradinas-sab'i wama aƙlalna, wa Rabbash-shayadini wama Adhlalna,wa Rabbar riyahi wama zaraina, fa inna nas'aluka khaira hazihil ƙaryati wa khaira Ahliha, wa na'uzu bika min sharriha wa sharri ahliha wa sharri ma fiha".** Albani ya inganta shi.

# Mataki na biyar

# 1

# Aƙida

«

**Tambaya ta 1:**

## shin ya halatta a yi yanka saboda wanin Allah?

**Amsa: 1**

## Ba ya halatta,

**ita ce kuma babbar shirka mai fitarwa daga Musulunci**

Dalili a kan haka faɗin Allah Maɗaukaki: ﴿**Ka yi sallah saboda Ubangijinka kuma ka yi yanka**﴾. **Suratul kausar (2).**

Da kuma Hadisin **Aliyu Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: Manzo Allah ﷺ ya ce:** **((Allah Ya tsine wa mai yanka saboda wanin Allah)).** **Muslim ne ya ruwaito.**

## 1 Aƙida

**Mataki na biyar: 5**

### Tambaya ta 2:

## Mene ne hukuncin sihiri?

### Amsa: 2

**Sihiri kafurci ne**, dalili a kan haka faɗin Allah Maɗaukaki: ﴿**Suna bin abin da shaiɗanu ke karantawa a kan mulkin Sulaiman, Sulaiman bai zama kafuri ba, sai dai shaiɗanu su suka kafirce, suna koya wa mutane sihiri, ba'a sauƙar da wasu Mala'iku guda biyu ba, a garin Babila Haruta da Maruta, ba sa karantar da kowa, bare ma su ce mu jarabawa ce kada ku kafirce**﴾. Suratul Baƙara (102).

## Tambaya ta3:

# Da me Musulmi yake rantsuwa?

## Amsa: 3

**Da suna daga cikin sunayen Allah, ko kuma wata siffa daga cikin siffofinSa**, an karɓo daga Abdullahi ɗan Umar ﵄, ya ce, lallai Annabi ﷺ ya ce: **((Duk wanda zai yi rantsuwa, to, ya rantse da Allah ko ya yi shiru)).** Bukhari ne ya ruwaito.

## Tambaya ta 4:

# Mene ne hukuncin rantsuwa da wanin Allah?

## Amsa: 4

**Rantsuwa da iyaye maza, ko da iyaye mata, ko da ɗaukaka, ko da ka'aba**, duk wata rantsuwa da wanin Allah haramun ne, Manzon Allah ﷺ ya ce: **((kada ku rantse da iyayenku maza, ko iyayenku mata, ko kuma gumaka, kada ku rantse sai da Allah, kuma kada ku rantse sai a kan gaskiya)). Albani ya inganta shi. Kuma Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Duk wanda zai yi rantsuwa kada ya rantse sai da Allah)).** Bukhari da Muslim ne suka ruwaito,

**Rantsuwa da wanin Allah shirka ce babba, idan ya yi ƙudurin cewa abin rantsuwar daidai yake da Allah wurin girma da ɗaukaka, idan ko bai yi haka ba to ƙaramar shirka ce.**

Tambaya ta 5:

## Mene ne hukuncin zagin Sahabbai?

Amsa: 5

## Duk wanda ya zagi Sahabbai gabaɗaya ko mafiya yawansu

**to ya kafirta, babu mai ƙinsu face kafiri, saboda su ne masu dakon shari'a, amma zagin ɗaya daga cikin Sahabbai, ko ɗaiɗaikunsu رضي الله عنهم ba kafirci ba ne, amma kuma fasiƙanci ne, mai aikata haka ya cancanci uƙuba ko kuma ya tuba.**

## Tambaya ta 6:

# Mece ce uƙubar wanda ya je wurin boka ko mai duba?

## Amsa: 6

# Ba za a karɓi sallarsa ba tsawon kwana arba'in

idan ya gaskata shi kuma ya kafurce wa abin da aka sauƙar wa Annabi ﷺ, dalili a kan haka Hadisin da aka karɓo daga wasu cikin matan Annabi ﷺ, daga Annabi ﷺ, ya ce: **((Duk wanda ya je wurin mai duba sai ya tambaye shi a kan wani abu, ba za a karɓi sallarsa ba tsawon darare arba'in))**. Muslim ne ya ruwaito. An karɓo daga Abu huraira رضي الله عنه daga Annabi ﷺ, ya ce: **((Duk wanda yaje wurin boka sai ya gaskata shi cikin abin da ya faɗa, haƙiƙa ya kafirce wa abin da aka saukar wa Muhammad ﷺ))**.

Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 7:

### Shin ya halatta a rataya laya?

## Amsa: 7

### Ba ya halatta

**saboda yana cikin layu waɗanda Annabi ﷺ ya hana a cikin faɗinsa: ((Duk wanda ya rataya laya, Allah kada ya cika masa, kuma duk wanda ya rataya 'yarwuri, kada Allah Ya bar masa alheri)).** A wata ruwaya: **((Wanda ya rataye laya haƙiƙa ya yi shirka)).** Albani ya inganta

## Tambaya ta 8:

# Mene ne Tawakkali?

## Amsa: 8

**Shi ne gaskiyar dogaron zuciya ga Allah, wurin neman biyan buƙata ko kuma tunkuɗe cutarwa, tare da aikata sabuba na shari'a**, dalili a kan haka faɗin Allah Maɗaukaki: **﴿Ga Allah zaku dogara in kun kasance Mumuninai﴾.** Suratul-Ma'idah (23). **Da Hadisin Umar ɗan khaɗɗab ﵁, ya ce: Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Lallai da zaku dogara ga Allah dogaro na gaskiya, da ya azurtaku kamar yadda yake azurta tsuntsu, zai fita babu komai a cikinsa, sai kuma ya dawo a ƙoshe)).** Albani ya inganta shi.

Tambaya ta 9:

## Mene ne hukuncin zagin Allah da ManzonSa da AddininSa?

Amsa: 9

### Kafurci ne babba

Dalili a kan haka faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: **﴿kace musu yanzu wa Allah da AyoyinSa da ManzonSa kuke wa izgilanci (65) Kada ku ba da uzuri, haƙiƙa kun kafirce bayan imaninku﴾.** Suratut-taubah (66-65).

1 **Aƙida**

**Mataki na biyar: 5**

**Tambaya ta 10:**

# Mene ne kafirci?

**Amsa: 10**

**Shi ne abin da ke kishiyantar imani cikin kuduri, ko magana, ko aiki,**

Allah Maɗaukaki yana cewa: ﴿**Duk wanda ya kafirce wa imani, haƙiƙa aikinsa ya rushe, kuma a lahira yana cikin hasararru**﴾. Suratul Ma'ida (5).

## Tambaya ta 11:

**Ka/ki ambaci matakan zunubai, sannan mene ne banbanci tsakanin babbar kafirci da karamar kafirci?**

## Amsa: 11

Banbanci tsakanin **kafirci babba** da **kafirci karami:**

### Karamin kafirci

- Ba ya cirewa daga musulunci.
- Ma'abocinsa ba ya dawwama a wuta
- Ba ya lalata ayyuka
- Yana iya haɗuwa da imani

### Babban kafirci

- Yana cirewa daga musulunci.
- Ma'abocinsa zai dawwama a wuta idan ya mutu a kai.
- Yana lalata ayyuka
- Ba ya haɗuwa da imani

## Tambaya ta 12:

**Shin ya halatta ga kowane Musulmi ya kafirtar ko ya fasiƙantar ko ya bidiantar da Musulmi?**

## Amsa: 12

### Ba ya halatta

**Ana barin lamarin kafirtarwa da fasiƙanctarwa da bidi'antarwa ga ma'abota ilimi ne, waɗanda suke sanin yaushe Musulmi zai kafirta, kuma yaushe zai yi ridda daga addininsa, kuma su gyara abin da ya kunshi gyara.**

## Tambaya ta 13:

# Mene ne abubuwa guda bakwai masu halakarwa?

## Amsa: 13

((Shirka da Allah, da sihiri, da kashe rai wanda Allah Ya haramta face bisa haƙƙi, da cin dukiyar marayu, da cin riba, da guduwa a lokacin yaƙi, da jifar mata masu kamun kai, masu gafala, Muminai)). Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

## Tambaya ta 14:

# Mece ce ingantacciyar aƙida game da Annabi isa ɗan Maryam ﷺ?

## Amsa: 14

**Lallai shi bawan Allah ne, kuma ManzonSa, kuma kalmarsa ce da ya jefa ta ga Nana Maryam**, kuma ruhi ne daga gare shi, Allah Yana cewa: **﴿Ya ku ma'abota littafi, kada ku wuce gona da iri a cikin addininku, kada ku faɗi magana game da Allah face ta gaskiya, lallai Masihu ɗan Maryam Manzon Allah ne, kuma kalmarsa ce wanda Ya jefa ta ga Maryam, kuma ruhi ne daga gare shi, don haka kuyi imani da Allah da ManzonSa, kada ku riƙa cewa su uku ne, ku hanu shi ya fi alheri a gare ku, Allah Shi kaɗai ne abin bauta da gaskiya, Ɗaya ne; Ya tsarkaka ace Yana da ɗa. Kuma abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nasa ne, kuma Allah Ya isa abin dogaro﴾**. Suratun-Nisa' (171).

Mataki na biyar: 5

# 2

# Tarihin Annabi ﷺ

## Tambaya ta 1:

# A kan wace dabba aka yi isra'i da Annabi ﷺ?

## Amsa: 1

**ita ce Buraƙ**

Dalili kuwa shi ne Hadisin Anas ɗan Malik رضي الله عنه, ya ce:

Annabi ﷺ ya ce: **((Sai aka zomin da wata dabba fara, ba ta kai alfadari ba girma, amma tafi jaki, ana kiran ta Buraƙ, sai na tafi tare da Jibrilu har muka isa saman duniya)).** Muslim ne ya ruwaito.

## Tambaya ta 2:

# Mene ne sunan Taguwar da Annabi ﷺ ya yi hijira a kanta?

## Amsa:2

# Sunanta Alƙaswa'u

Dalili a kan haka shi ne Hadisin da Bukhari ya kawo a babin taguwar Annabi ﷺ, daga Ibnu umar رضي الله عنه: **Manzon Allah ﷺ ya goya Usama a kan taguwarsa Al'ƙaswa'u.** Bukhari ne ya ruwaito.

**Tambaya ta 3:**

## Wane masallaci ne Annabi ﷺ ke kai wa ziyara duk rana ta Asabar a kan abin hawa ko da ƙafa?

**Amsa: 3**

# Masallacin ƙuba'

Dalili a kan haka Hadisin ɗan Umar رضي الله عنه, ya ce: **"Manzon Allah ﷺ ya kasance yana zuwa masallacin ƙuba' kowace ranar Asabar a kan abin hawa ko da ƙafa", kuma shi ma Abdullahi ɗan Umar ya kasance yana aikata haka.** Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

## Tambaya ta 4:

# Mace ce falalar Salla a cikin masallacin ƙuba'?

## Amsa: 4

**Ita ce** **ladar umra**, dalili a kan haka abin da ya tabbata daga Manzon Allah ﷺ, lallai ya ce: **((Wanda ya yi tsarki a gidansa, sannan ya taho masallacin ƙuba' ya yi salla a cikinsa, yana da lada ta umra)).** **Albani ya inganta shi.**

## Tambaya ta 5:

**Su waye ne sahabbai guda goma da aka musu bishara da Aljannah:**

## Amsa: 5

**Sune: Khalifofi shiryayyu guda hudu.**

**Abubakar Siddiƙ**

**Umar ɗan Khaddab**

**Usman ɗan Affan**

**Aliyu ɗan Abu Ɗalib**

**Ɗalhatu ɗan Ubaidullahi**

**Zabairu ɗan Awwam**

**Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas**

**Sa'id ɗan Zubair**

**Abdurrahman ɗan Awf,**

**da Abu Ubaidata ɗan Jarrah رضي الله عنهم**

## Tambaya ta 6:

**Wane ne ya yi wa Annabi ﷺ sihiri?**

## Amsa: 6

**Shi ne Labid ɗan A'asam bayahude**

Dalili a kan haka Hadisin Aisha رضي الله عنها, ta ce: **((Wani mutum ya yi wa Annabi ﷺ sihiri daga cikin kabilar Zuraiƙ, ana kiran sa Labid ɗan A'asam)).** Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

## Tambaya ta 7:

## Waɗanne yaƙoƙi ne suka fi shahara a cikin yaƙoƙin Annabi ﷺ?

### Amsa: 7

Mafiya shahara su ne:

**Yaƙin Badar**

**Yaƙin Uhud**

**Yaƙin Khandaƙ**

**Yaƙin Khaibar**

**Yaƙin Mu'utata**

**buɗe Makka**

**Yaƙin Hunain**

**Yaƙin Tabuka.**

**Tambaya ta8:**

**Waɗanne Sahabbai ne Annabi ﷺ ya naɗa su jagorori a yaƙin Mu'ta?**

**Amsa: 8**

Su ne:

**Zaidu ɗan Harisa**

**Ja'far ɗan Abu Ɗalib**

**da Abdullahi ɗan Rawaha**

Allah Ya ƙara musu yarda.

## Tambaya ta9:

# Yaushe aka yi yaƙin Badar da Uhud da Khandaƙ?

## Amsa: 9

**An yi yakin Badar ne a**
shekara ta biyu bayan hijra
**Adadin Musulmi**
Mazaje ɗari uku da goma sha bakwai
**Adadin mushirikai**
Mayaka dubu

**Yaƙin Uhud kuma an yi shi a**
A shekara ta 3 bayan hijira,
**Adadin Musulmi**
mayaƙa dubu
**Adadin mushirikai**
Mayaƙa dubu uku

**Shi kuma yaƙin Khandaƙ an yi shi ne a**
A shekara ta 5 bayan hijirah
**Adadin Musulmi**
mayaƙa dubu uku
**Adadin mushirikai**
Mayaƙa dubu goma

## Tambaya ta 10:

# Yaushe aka yi waɗannan yaƙoƙi masu zuwa, Yaƙin Khaibar, Yaƙin Mu'ta, Yaƙin Hunain da Tabuka.

## Amsa: 10

**Yaƙin Khaibar**
A shekara ta 7 bayan hijira
Adadin Musulmi: Mayaƙa dubu da ɗari huɗu

**Yaƙin Mu'ata**
A watan Jumada Ula Shekara ta 8 bayan hijira
Adadin Musulmi: Mayaƙa dubu uku
Adadin mushirikai: Mayaƙa dubu ɗari biyu

**Yaƙin Hunain**
A watan Shawwal shakara ta 8 bayan hijira
Adadin Musulmi: Mayaƙa dubu sha biyu
Adadin mushirikai: Mayaƙa dubu ashirin

# Mataki na biyar: 5



**Yaƙin Tabuka**

A watan Rajab shekara ta 9 bayan hijira

**Adadin Musulmi**

**Mayaƙa dubu talatin**

**Adadin mushirikai**

**Mayaƙa dubu arab'in**

# 3

# Zikirori na Shari'a

## 3 Zikirori

**Mataki na biyar: 5**

### Tambaya ta 1:

# Me za ka ce idan za ka shiga kasuwa?

### Amsa: 1

**Zan ce: "La ilaha illahu wahdahu laa sharika lahu, lahul mulku wa lahul hamdu, yuhyi wa yumitu wa huwa hayyun laa ya muutu, biyadihil khairu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadir".**

**'Wanda ya shiga kasuwa sai ya ambaci wannan zikiri Allah Zai rubuta masa lada dubu sau dubu, ya kuma shafe masa kurakure dubu sau dubu, Ya kuma ɗaukaka darajarsa dubu sau dubu, kuma Ya gina masa gida a cikin Aljanna.** Albani ya inganta shi.

## Tambaya ta 2:

# Me za ka ce idan ka sauƙa a wani masauƙi a halin tafiya ko kuma ka sauya wuri?

## Amsa: 2

**Zan ce:** "A'uzu bikalimatillahit tammat min sharri ma khalaƙa" An karɓo daga Khaulatu 'yar Hakeem ﵂, ta ce: **Na ji Manzon ﷺ yana cewa: ((Wanda ya sauƙa a wani masauƙi sai ya ce: "A'uzu bikalimatillahit tammat min sharri ma khalaƙ", wani abu ba zai cutar da shi ba har ya bar wannan masauƙi na shi)).** Muslim ne ya ruwaito.

## Tambaya ta 3:

**Akwai wasu kalmomi guda biyu marasa nauyi a kan harshe, masu nauyi a kan mizani, masu soyuwa a wurin mai Rahama,
Wađanne kalmomi ne su?**

## Amsa: 3

# "Subhallahi wabi hamdihi subhanallahil Azim"

An karɓo daga Abu Huraira رضي الله عنه, ya ce: **Manzon Allah ﷺ ya ce: ((Kalmomi guda biyu marasa nauyi a kan harshe, masu nauyi a kan mizani, masu soyuwa a wurin Mai Rahama, "Subhallahi wabi hamdihi subhanallahil Azim")).** Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.

Tambaya ta 4:

## wace addu'a ake faɗa a daren Lailatul Ƙadari?

Amsa: 4

Ana cewa: **"Allahumma Innaka Afuwwun tuhibbul afwa fa'fu anni".** An karɓo daga A'isha ﷺ, ta ce: Na ce: **Ya Manzon Allah ﷺ! Ba ni labari, idan na dace da daren lailatul ƙadari, me zan ce? Ya ce:** za ki ce: **((Allahumma Innaka Afuwwun tuhibbul afwa fa'afu anni)).** **Albani ya inganta shi, Allah Ya yi masa rahama.**

Tambaya ta 5:

# Me za ka ce bayan kiran sallah?

Amsa: 5

## Zan faɗi kwatankwacin abin da mai kiran Salla yake faɗa

Sannan na yi sallati wa annabi ﷺ. An karɓo daga Jabir رضي الله عنه cewa: Lallai Manzon Allah ﷺ ya ce: **((Duk wanda ya ce a lokacin da ya ji kiran salla: "Allahumma rabba hazihid-da'awatit tamma, was-salatil ƙaimati, A'ti Muhammaɗanil wasilata wal fadilata, wab'ashu maƙaman mahmuɗanillazi wa'adtahu", cetona ya halatta gare shi ranar ƙiyama))** Bukhari ne ya rawaito.

## Tambaya ta 6:

# Mece ce addu'ar buɗe Salla?

## Amsa: 6

## Ita ce addu'a da ake yi bayan kabbara ta harama kafin Fatiha.

An karɓo daga Abu huraira ﵁: Manzon Allah ﷺ ya kasance yana shiru tsakanin kabbara da fara karatu na ɗan wani lokaci - ya ce: ina tsammani ya ce: lokaci ɗan kaɗan - sai na ce da shi: **Fansar mahaifina da mahaifiyata ya Manzon Allah, shiru da kake yi tsakanin kabbara da fara karatu me kake cewa? Sai ya ce: ina cewa:** **((Allahuma baa'id baini wa baina khaɗayaya, kama ba'adta bainal mashriƙi wal magribi, Allahumma naƙƙini minal khaɗaaya kamaa yunaƙƙas-sabul abyadu minad-danas, Allahummagsil khaɗayaya bil maa'i was-salji walbaradi)).** **Bukhari da Muslim ne suka ruwaito.**

Tambaya ta 7:

# Mece ce siffar ruƙya ta shari'a?

Amsa: 7

Daga Ayoyin Ƙur'ani mai girma ana yin ruƙya da: Karanta Fatiha, da Ƙula'uzai, da Ayatul Kursiyyu, Ƙur'ani gabaɗayansa ma waraka ne.

Daga addu'oi na Sunna kuma akwai:

((Allahumma rabban na's, azhibil ba'as, ishfi antash shaafi, laa shifa'a illa shifa'uka, shifa'an laa yugaadiru saƙaman)). Sau uku.

((Bismillahi Urƙika, min kulli shai'in yu'uziika, wa min sharri kulli nafsin au aini ha'sidin, Allahu yashfiika, bismillahi urƙika)).

"Bismillahi" (sau uku), sannan ya ce: "A'uzu bi

izzatillahi wa ƙudratihi min sharri ma ajidu wa uha'ziru", sau bakwai (7).

((A'uzu bikalimatillahi min kulli shaiɗanin wa hammatin, wa min kulli ainin lammatin)).

Sai ya yi tofi wa marar lafiya a in da yake masa ciwo, kuma ya yi masa addu'a yana masa tofi da yawunsa. Ya karanta fatiha ya maimaita sau bakwai (7), ya karanta ayatul ƙursiyyu, sai ya karanta abin da ya sawwaka daga Ƙur'ani, sannan ya karanta: ((ƙulhuwallahu ahadun)) da ƙula'uzai guda biyu ya maimatasu sau uku (3), sai ya yi tofi da su, ya kuma roƙi Allah.

Tambaya ta 8:

## Mene ne lokacin zikirin safiya da na maraice?

Amsa: 8

**Lokacin zikirin safiya shi ne:**
**Bayan salla ta asubahi zuwa fitowar rana**
**lokacin zikirin maraice kuma shi ne:**
**Bayan sallar la’asar har zuwa faɗuwar rana**

kuma lamarin wannan zikiri na da yalwa (zaka iya yin su a wasu lokuta ba wannan ba).

DON TUNTUBAR MU:

salahasalem@yahoo.co.uk
00218 91 849 1000
00966 57 784 4347
@knzbooks